Ku yawaita tina mai rushe jin daɗi". Yana nufin mutuwa

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Ku yawaita tina mai rushe jin daɗi". Yana nufin mutuwa.
[Hasan ne] [Tirmizi da Nasa'i da Ibnu Majah ne Suka Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kwaɗaitar akan yawaita tinanin mutuwa, da tinaninta ne mutum yake tuna lahira, kuma soyayyarsa ga duniya ta rushe a cikin zuciyarsa, musammanma dai abubuwan da aka haramta.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66232